# KAFA

# IKILISIYA

## Gabatarwa Na Koyarwa



GLOBAL ADVANCE

# 1. ME YA SA AKE KAFA IKILISIYA?

(Kimanta lokacin koyaswa mintoci 30)

A. Ikon hades ba zata rinjayi Ikilisiya ba (Matta 16:18)

Matta 16:18 ita ce karo na farko da a ka ambaci kalmar ikkilisiya a Sabon Alkawari. Kalmar nan Ikkilisiya Kamar yadda Yesu ya yi amfani da ita an samo asalinta ne daga Kalmar Hellenanci “ekklesia” ma’ana “kirayayyu” ko “taron jama’a”. Watau ikilisiyar da Yesu ke magana a matsayin ikilisiyarsa ita ce taron jama’a wadanda a ka kira su daga duniya ta wurin Bisharar Almasihu.

Yesu ya nanata gaskiyar cewa ikon mutuwa ba zata iya dauke shiba (rinjayar sa) . Ba Wai kawai za’a kafa ikilisiya (jikin/jama’ar Almasihu) duk da ikon Hades ko jahannama ba, amma Ikkilisiya zata bukasa duk da wadanan ikokin. Ikilisiya ba za ta taba kasawa ba, ko da yake tsara zuwa tsara zata mika wuya ga ikon mutuwa ta jiki, duk da haka wasu tsarraraki za su taso don su rayar da ikilisiya. Kuma za ta ci gaba har sai ta cika aikinta a wannan duniya kamar yadda Yesu ya umarta (Matta 28:18-20).

Wannan yana ba mu tabbaci (karfin hali) a cikin kokarinmu na kafa ikilisiya! Ko da a tsakiyar yake-yake na ruhaniya da kuma wahala, nufin Allah zai yi nasara a ƙarshe. Za mu iya kasancewa da tabbatacin taimakonsa yayin da muke bin jagorancinsa.

B. Daya daga cikin Manyan hanyoyin auna ci gaban Bishara da kuma cikamakin Babban Umarni

Bincike na yanzu ya nuna cewa tare da karuwar yawan mutane a duniya, ana bukatar kimanin sababbin ikilisiyoyi miliyan 5 a cikin shekaru 5-10 masu zuwa don kawai a cigaba da tafiya. Yawan al’ummar duniya a halin yanzu kusan mutane biliyan 7 ne. Nan da shekarar 2050, da alama adadin zai karu zuwa kusan biliyan 11. Yayin da adadin mutane ke karuwa, haka ma bukatar yawan ikilisiyoyi ta kasance don kai bishara ga batattu.

C. Babban burin Babban Hukumar ( umurni)  ya kamata ya zama Ikilisiya domin kowane mutane wanda ya zama tushen isar da Bishara ga kowane mutum. (Romawa 15:9)

> Romawa 15:9 na bayyana cewa ya kamata hakkinmu ya zama kafa ikilisiyoyi a tsakanin Al'ummai. Kalmar Al'ummai ya samo asali ne daga harshen Hellenanci "ethnos" ma'ana, kowace al'umma da jama'a. Har sai kowace rukunin jama'a a duniya da ba ta ji bishara ba ta ji bishara, aikinmu bai cika (kammalu) ba. Annabci ta nuna cewa za a sami masu bi (krista) daga kowace rukunin jama'a da za su taru a gaban kursiyi.

D. Ikilisiya ita ce bayyanar abin da zai zo (auku) a gaba – Mulkin Allah da ke iko bisa duniya (Zabura 96:3)

> Ikilisiya bayananniyar wakiliya ce na  sarauta, iko da Mulkin Kristi a cikin aiki na yau. Duk da matsaloli da rashin tabbas, ikilisiya za ta zama wadda ke bayyana manufofin Allah. Saboda wannan dalili, Allah yana kishi domin ikilisiyar Sa haka ya kamata mu ma masu kafa ikilisiya mu tuna cewa ikilisiya amarya ce na Kristi kuma dole ne a bi da ita yadda ya kamata.

E. Ikilisiyar na duk fadin duniya ta kunshi dukan mutanen da aka fansa daga kowace al'umma (kasa) wadanda suke da'awar Yesu Kristi a matsayin Mai Cetonsu da Ubangiji. Don haka kowace rukunin jama'a na duniya na bukatar wasu nau'i na ikilisiya (Romawa 1:5).

> Manzo Bulus ya nuna a cikin Romawa 1:5 cewa mun Sami alheri, bishewa, da kuma al' hakin shugabanci don kafa mulkin Allah a cikin kasashe na duniya.

F. Ikilisiya ita ce amaryar Kristi wanda Kristi Zai sake dawowa domin ta. (Ruya ta Yohanna 19:7-9, 2 Kor. 11:2)

> Yesu yana jiran amaryarsa ta cika nufinta. Yana neman amarya tsatsarka, marar aibi, da ta kunshi mutane daga kowace al'umma . Harshe (yare) da aka yi amfani da ita a 2 Korantiyawa 11:2 na nuna cewa yana marmarin daukar amaryarsa. Da babban sammani Yana jiran ikilisiya ta kasance cikin shiri!

Duk da haka, Kristi ba zai dawo ba har sai an kammala girbin. Tun da yake babu wanda ya san sa’ar (Matta 24:26), a matsayin mu na ma’aikata masu girbi; mu ci gaba da yin aiki da kwazo har sai Mai Cetonmu ya dawo.

## II. TSARI DA LOKACIN KAFA IKILISIYA

(kimanta lokacin koyaswa mintoci 45)

A. Kafa ikilisiya tsari ne.


Yayen da ka zabi ka saurara ka kuma amsa (yin na'am) ga jagorancin Ubangiji a kafa ikilisiya, yana da muhimmanci a fahimci cikakkun bayani da suka kunsa. Ko da yake tsarinka zai kasance da bambance bambancen da suka shafi al'adarku, abin da ka ke hari da kuma hangen nesan ka don kafa ikilisiya– akwai wasu mahimman matakai wadanda keda mahimmanci kuma sunyi dai-dai da duk tsarin kafa ikilisiya.

Ya na da muhimmanci ka tabbatar cewa ba ka tsallake wadanan matakan nan ba a kokarin kammala aiki cikin sauri. Idan an yi abubuwa cikin sauri( da gaggawa) to mai yiwuwa ne ikilisiyar ta yi fama ( gwagwarmaya) kuma za ta zama mara karko( rashin kwanciyar hankali) a tafiyar. Yi la'akari da tsari da kwakwaran abubuwa da suka zama wajibi cikin tsari mai karfi ko gini da zai iya jure wa iska, ruwan sama, guguwa har ma da girgizar kasa. Idan ba a saka harsashen yadda ya dace ba ginin za ta ruguje. Wannan misali ne na bayyanannen wakilcin yadda yake da muhimmanci a rungumi tsari na kafa ikilisiya.

Ta wannan horon za mu tattauna ainihin ka'idodi na Sabon Alkawari da za ta bamu cikkaken tsari wanda zamu iya zuba ido akai.

B. Bangarori na Tsarin Kafa Ikilisiya

**AIKIN YI A RUKUNI:**
Ka sa masu kafa ikilisiya su yi ma'amala da kai mai gabatarwa a taimakawa ga tsara zane da wasu kanshin gaskiya na kansu masu sarkakiya da za su iya tunani suke da mahimmanci wajen kafa ikilisiya. Wannan zai ba wa malamai damar kimanta inda masu kafa ikilisiya su ke a cikin Littafi Mai Tsarki da kuma kuma fahimta a auikace na




Ci gaba da horaswar mu za mu tattauna abubuwa masu tsamari (sarkakiya) na:


- Dalilin da yasa muke bukatar kafa ikilisiyoyi.
- Izawa domin kafa ikilsiiyoyi.
- Kima, Hange nesa da kuma Salo domin kafa ikilisiyar ka ta gaba.
- Shiri da Dabara domin kafa ikilisiya
- Habaka kungiyarka domin tsarin kafa ikilisiya
- Shelar bishara da kuma yin nasara da makiyi (yaki na ruhaniya)
- Almajirantar da mutane su shagaltar da duniya ta bangarorin tasirin su.

B. Fahimtar Lokuta da yanayi don kafa Ikilisiya.

Kari akan aikatacciyar hanyar kafa ikilisiya ya wajaba ka yi la'akari da yanayin ruhaniya da kuma yanayin tunani da watakila zaka ci karo da su. Tsarin kafawa ba ta zarce (wuce) dukan sauran bangarorin ba.

Yanayi (lokutan) kafa ikilisiya za su kai ka daga kololuwar dutse mai tsawon ( marmari mai anashuwa) dandanawa zuwa ga kwararruka na kasa mafi wahala da ka taba dandanawa.

Masu kafa ikilisiya suna matsawa daga **Hange** zuwa **Yin Tsari** da kuma **dabara** daga nan su cigaba zuwa ga dukan burin su. Duk da haka, a wani wuri cikin tafiyar hakika za a fuskanci **Cikas (matsaloli)** da za'a iya fuskanta. Matsalar ba shine cikas din ba ne, amma yadda za ka magance wannan Cikas din ne. Zabi zai zama naka don ka jure cikin cikas da ta same ka don ka dandana nasara ko kuma ka fuskanci yanayi na **hargitsi.** Ta wurin alherin Allah za ka jure ka ci gaba har zuwa ga **Yin murna (shagali).** Idan ka tsinci kanka a cikin wani yanayin **hargitsi (rikici),** abokin gaba zai yi kokarinsa ya kadaita(ware ka daga saura) ka ya kuma kawo ka zuwa wurin **Gajiyarwa.** Da zarar ka gano ( fahimci) kanka a cikin wannan yanayi, ka yi iya kokarinka don gaggauta mika kanka (da kuma iyalinka) zuwa tsari na **warkaswa da kuma Maidowa (rayarwa)!**




C. Fadakarwa na (Sanin) Yanayi/lokaci

Masu kafa ikilisiya da dama sun fara tafiyar da marmari suna jin kamar za su iya mamaye duniya. Yayen da wannan na iya zama daya daga cikin tafiya mafi farin ciki da za su dandana, ana bukatar yin la'akari da lokuttan kafa ikilisiya. Mai yiwuwa a cikin watanni shida zuwa shekara daya mai kafa ikilisiya zai fuskanci cikas wanda zai kai ga rikici/hargitsi a gaba.

Domin samun ci gaba a cikin yanayi na kafa ikilisiya, yana da muhimmanci a gano wane mataki ne ka ke fuskanta da kuma aiki a ciki. Yanayi na kafa ikilisiya na iya maimaitawa da sauri ko a hankali. Bugu da kari mai kafa ikilisiya na iya tafiya ta zagayowar yanayi da yawa a cikin tsawon lokaci na kafa ikilisiya. Fahimtar hakan zai taimake ka daga yin sanyin gwiwa idan kana cikin yanayin tashin hankali (hargitsi), gajiyarwa/kadaici, ko waraka da kuma sabuntawa. Ka Karfafa kanka daga cikin Mai Wa'azi 3:1-8 ka kuma

tuna cewa komai yana da lokaci, kuma kamar lokaci masu cikawa, lokacinka hakika za ta ci gaba zuwa  gaba.

## III. MA'ANA DA KUMA MANUFAR IKILISIYA?

(Kayadadden Lokacin Koyaswa mintoci 30)

A. Ikilisiya taruwan masu bi ne (Krista) saboda manufa ta Littafi Mai Tsarki na yin sujada, addu'a, koyo da kuma aikin bishara. Kalmar ikilisiya an samo ta ne daga kalmar ekklesia, wadda ake nufi da taron jama'a ko kirayayyu daga duniya. (Matta 21:13, Zabura 1501-6).

Yesu ya bayyana a fili cewa ikilisiya ya kamata ta zama wuri ne na yin addu'a. Ko da yake ikilisiyoyi suna da shirye-shirye da dama da kuma ayyuka da yawa, babban dalilin taruwar masu bin Krista ya kamata ya kasance domin yin addu'a, sujada da kuma kusanci da Allah.

Shafi a cikin Zabura 150:1-6 ya ba da wani kwatanci da ke nuna halinmu da ayukanmu. Yabo, daukaka da girmama Allah suna da matukar mahimmanci. Yayen da masu bi za su karaya a zuciya, matsayi da halin yabo ga Allah nan da nan zai rage damuwowi na duniya ya kuma sake kai hankalin mu ga Mai Iko Duka.

B. Yesu ne shugaban ikilisiya, wanda ita ce jikin Kristi (Afisawa 1:22-23)

Dole a ba da ma'anar Manufar kasancewar ikilisiya ta kuma nuna Yesu wanda shi ne shugaba ga dukkan abubuwa. Ya zabe ka domin babban aiki na kafa ikilisiya. Ko da yake, shi ne mafari da cikar dukan abubuwa. Shi ne yake bi da mutane, jagorantar su yana kuma jawo mutane zuwa ga Uba. Kada ka yarda girman kai ta shiga cikin zuciyarka domin aikin da ya kira ka ga yi aiki ne mai girma da ban sha'awa.

Tunatar da kanka cewa Kristi shi ne shugaba hakan zai ba ka kwarin gwiwa da tabbacin cewa kai mai kula da shirin sa ne. Babban Hakki (nawaya)ne a kula da wani abu saboda Ubangiji, muna kuma samon goyon baya da taimako daga wanda shi ne shugaban ikilisiya yadda muke bukata.

C. Jikin Kristi ya kunshi dukan masu bi cikin Yesu Almasihu tun daga ranar Fentekos (Ayyukan Manzanni sura 2) har zuwa dawowar Kristi. Jikin Kristi ya kunshi bangarori biyu:

1. Ikilisiya ya duniya baki daya (ikilisiyar gama-gari) ta kunshi duk wadanda ke da dangantaka da Yesu Kristi (I Korantiyawa 12:13).

   Duniya na iya kasancewa da tsari na aji ko kabila, amma babu wani abu kamar haka a ikkilisiya gaba daya. Dukan mutane da ke da danganataka da Yesu su gabobi ne na jikin. Komai arzikin ka, talauci, matashi ne, tsoho ne, mai ilimi, ko mara ilimi – Allah ba ya duban mutum ta wannan hali. Muradin Sa shine dangantaka da kuma mika kai a gare Shi.

2. An kwatanta Ikilisiyar yanki (gida) a cikin Galatiyawa 1:1-2: “Bulus, manzo… da dukan ‘yan’uwa da suke tare da ni, zuwa ga ikilsiyoyin kasar Galatiya”. Anan mun ga cewa a yankin Galatiya akwai ikilisiyoyi da dama – abin da muke kira ikilisiyu na gida.

A matsayin ka na mai kafa ikilisiya, Allah ya zabe ka ka zama daya daga cikin wakilan sa a inda kake, kuma duk da haka kai bangare ne na ikilisiyar duniya gaba daya (ikilisiyar gama-gari). Kafa Ikilisiyarku wani sashe ne na jikin Kristi a duniya baki daya, har ma da na inda ka ke. Kari da haka, kowane mutum a cikin ikilisiya inda ya ke yana da babbar rawar da zai taka (aikin yi) a cikin ikilisiyar. Dukan ikilisiyoyi da dukan mutane a cikin ikilisiya suna da muhimmanci.

D. Abin da ba ita ce ikilisiya ba

1. Gini.
2. Darika.
3. Fili.
4. Kasuwanci/sana'a.
5. Wurin nishadi (shagali).
6. Wurin hidimar kungiya ta jama’a

Ko da yake akwai daraja cikin gine-gine, fili, albarkatu da zamantakewar jama’a, ba nufin ikilisiya ba ne kuma kada a dangata ma’anarta (ikilisiya) daga cikin wadannan abubuwa. Za a iya ba da ma’anar Ikilisiya kadai a kuma dube ta a matsayin rukunin mutane da ke taruwa domin sujada, yin addu’a, bincike da aikin bishara.

A matsayin shugaba mai hangen gaba zai zama wajibinka ka bada daraja da ya dace wa ikilisiya ka kuma ware (raba) sauran abubuwan nan daga manufar ikilisiyarku. Jama’a a yanzu sun zama mazaunin (wurin zaman) Ruhu Mai Tsarki, Ubangiji ba ya zama kuma a ginin haikali a duniya.

## IV. MURADIN KAFA IKILISIYA

(kayyade Lokacin koyaswa mintoci 60)

A. Muradi domin kafa ikilisiya dole ta zama amsa ga hangen ka da kuma amsa kira daga Allah.

1. Wannan a kullum ita ce mataki na fari. Dole Allah ya ba ka hasken abin da yake so a kammala. Wahayi (hange) na iya zuwa daga cikin Nassi, mafarki, tabbataswa daga wajen wasu, annabci, ko nawayya da ta sha maka zuciya domin wani wuri ko rukunin mutane (Ayyukan Manzanni 13, Ayyukan Manzanni 16:9-10).

Wasu masu kafa ikilisiya da farko su kan yi na'am da kiran Allah, amma daga nan sai su kauce. Wasu suna kafa ikilisiya bisa ga son biyan bukatan kansu. Wasu masu kafa ikilisiya suna farawa bisa ga amsa kiran Allah, amma daga nan sai a janye su ta wurin son yin nasara (nasara ta mosta su).

Mutane wadanda ake janyewa su ne:

a. Masu gamsuwa da abubuwan da suka kammala( nasara akai)
b. Wadanda alamu na cin nasara na mallakar su, (yin suna, arziki, iko, hikima ta duniya).
c. Masu rashin mutunci, (kazamta, sonkai, girman kai, bukatar abu).
d. Masu son yin gasa sosai, (2 Kor. 10:12).
e. Rashin daidaita aiki da lokaci yadda ya kamata (Luka 10:41-42).
f. Suna son sadakar da dangantakarsu don aiki.

2. Idan hangen, kira ko dalili na kafa ikilisiya bai samo asali daga Allah ba, ba shakka za a fuskanci faduwa (kasawa). Sanin cewa an kira ka ba shi ne kawai kyakkawan ra'ayi ba. Abu ne wanda hakika yana da matukar muhimmanci (Zabura 127:1)

Kira aiki ne na Ruhu Mai Tsarki, amma janyewa (kaucewa) aiki ne na jiki. Hange, kira ko Muradi dole a kullum ya zama a kafe a cikin yin na'am da Ruhu Mai Tsarki.

B. Fai'dodin sanin cewa an kira ka.

1. Mayarda hankali ga manufa ta wurin zama mai tarayya (mai hadin kai). (I Korantiyawa 3:9)

A matsayin mu na abokin tarraya muna da izawa na Ruhu Mai Tsarki da kuma taimako don cika wahayin (hangen). Aiwatarwa da ikon kanka ba tare da Ruhu Mai Tsarki ba ya zama matsayi ne na zato da kuma kebewa (janye kanka). Kari ga haka, halin fahariya ne da sonkai. Masu hada hannu suna dogara ne ga Ruhu Mai Tsarki, kuma ba masu sonkai ba ne, ba su tara abu don kansu ko nemar wa kansu girma domin nasarar su.

2. Albarku da kuma Tanadi (Filibiyawa 1:3-6).

Wasu sun ce, "Inda bishewar Allah ya je, yakan tanada," sa'annan wasu sun ce, "Allah yana biyan abin da ya umarta a yi". Wadannan maganganu suna wakilta kuma suna tabbatar da amincin Allah da tanadin Sa. Sunan Allah "Yahweh Jireh" a cikin Farawa 22:14. Ma'anar sunan shi ne "Ubangiji wanda yake Gani, ko Ubangiji wanda Zai yi Duba Game Da Abin." Tanadi da kuma albarka suna nan a yalwace kuma alkawari ne ga wadanda ke tafiya cikin biyayya ga Allah.

3. Bangaskiya da jurewa ta wurin gwaje-gwaje (Ibraniyawa 12:1-3, 2 Tasalonikawa 3:5, Yakubu 1:2-4).

Kokarinmu don aikata kamun kai bisa ayyukanmu da kuma yin tsayayya da jarabobin yin zunubi ba zai taba zama cikakken nasara ba a nan duniya. Mudin muna rayuwa a matsayinmu na 'yan adam, za mu yi gwagwarmaya da faduwa da kuma zunubi kowace rana. Dole ne mu tuna cewa kasawa ba yana nufin karshen amfaninmu ba ne. Kristi yana da cikakkiyar fahimtar kasawarmu, kuma cikin Sa muna iya samun sabon jinkai kowace rana (Ibraniyawa 4:14-16), Makoki 3:22-23). Matukar muka furta kuma muka tuba daga zunubanmu da kuma kasawanmu, Allah ya yi alkawarin zai tsarkake mu, ya warkar da mu, ya kuma maido da mu (I Yohanna 1:9).

Bulus ya rubuta "… kada mu yi sanyi da yin aiki nagari, don za mu yi girbi akan kari, in ba mu karai ba" (Galatiyawa 6:9). Kome wuyar hali da kake ciki, kada ka karaya game da

manufar Allah don ya ba ka nasara har zuwa karshe. Ka Jure, kana zuba ido ga Kristi ya taimake ka  a kullum wannan gwaje-gwaje za su gina jurewarka, kuma jurewarka za ta sa ka da kuma hidimarka duka zuwa ga zama shaida masu karfi na bangaskiya.

C. Rungumar kira da kuma hangen nesa don kafa ikilisiya.

1. Ubangiji na iya kiranka zuwa ga kafa ikilisiya ko ka “ka yi na’am(karba) ko ba ka yi ba.
    a. An kira Musa don ya hidimta daga ‘jeji (kurmi) mai cin wuta.
    b. Gideon sa’adda ya ke sussukar alkama.
    c. Yunanah Allah ya kira shi don ya tafi Ninevah ya yi shelar wa’azin tuba. Duk da haka, Yunanah ya yi kokarin ya gudu daga fuskar Allah da kuma kira ga yin biyayya.
    d. B iyayya ya fi hadaya. (I Sama’ila 15:20-26)

2. Yi addu’a domin hikima da yin sahihiyar tambayoyi ga Ubangiji (Yakubu 1:5, 6b)
    a. Tambayi Allah idan ya na umurtaka ga kafa ikilisiya.
    b. Tambayi Allah inda yake jagorantarka don ka kafa ikilisiya
    c. Tambayi Allah lokacin da yake so ka kafa ikilisiya.
    d. Tambayi Allah yadda yake bishe ka don ka kafa ikilisiya.

Allah ba ya jin tsoron tambayoyin ka, kuma bai jin tsoron ya amsa maka. Sau da yawa muna kasa yi wa Allah tambayoyi da suka dace domin haka amsarmu ga kiransa kan kauce hanya. Ko ma manzo Bulus an bi da shi masamman ta wajen jagorancin Ruhu Mai Tsarki zuwa Makidoniya. Wannan ba Shirin Bulus ko manufar sa ba ne, amma Allah ya nuna a fili da cewa ya kamata ya tafi ya ziyarci wani mutum mai suna Karniliyus. Ta wajen jagorancin Ruhu Mai Tsarki, an sami mutumin a shirye, yana jira ya karbi Bishara. Neman bayani don kwatanci da hikima nada muhimmanci.

3. Nemi shawara daga mutane masu tsoron Allah, zai fi kyau daga wajen mutane guda uku ko hudu. (Misalai 11:14)
    a. Ka tabbata a kalla biyu daga cikin su suna da kwarewa a kafa ikilisiya da kuma aikin fasto na ikilisiya.
    b. Nemi haske game da abinda suke gani a matsayin karfinka da raunin ka yayen da an zo zancen kafa ikilisiya.

Shawarwari da hikima daga gogaggun shugabanai da yawa zasu iya ceton ka daga kaucewa wa bakin ciki da kuma taimaka maka wajen guje wa matsaloli. Mutanen da suka rigaya suka yi tafiya ta hanyar kafa ikilisiya zasu iya shaida hikimar su da kuma nasarar su da gazawar su.

Ka yi saurin sauraro, amma ka yi addu'a cikin la'akari domin shawarar da aka ba ka kafin ka aikata (Yakubu 1:19). Kamar yadda wasu zasu iya nuna yuwuwar faduwa ko raunin da suke gani a rayuwar ka, ka kasance da tawali'u da karbuwa. Kada ka yi fushi idan ba ka son shawarar da aka ba ka, amma cikin addu'a ka mika shawarwarin ga Ubangiji daga nan roke shi domin tabbatarwar sa da kuma wahayi.

4. Yi addu'a da azumi, ka bar Allah ya bishe ka bisa ga yanke zabin ka (yanke shawarar ka). (Ayyukan Manzanni 13).
    a. Roki Ruhu Mai Tsarki ya yi magana da kai (Yohanna 14:26a).
    b. Kada ka matsa, aikata ko kuma ka kirkiro naka kiran!

Addu'a irin wannan za ta fitar da sakamako masu iko (karfi). (Ezra 8:21-23, Ishaya 58:6). A cikin dukan Tsoho da Sabon Alkawari, azumi da addu'a sammanci ne na ladabi kuma a kullum su na gaban manyan nasarori.

Musa ya yi azumi akalla kwana arba'in har sau biyu. Yesu ya yi azumi na kwanaki arba'in. Ya kuma fada wa mabiyansa su yi azumi. Sarki Dawuda ya kaskantar da kansa ga yin azumi. Masu bi ana karfafawa da a yi azumi domin a iya ganin nasara da yin cikaken dangantaka da Yesu, da kuma samun canji, falkawa na kanka da kuma ganin ikon Allah.

Addu'a da yin azumi wajibin abu ne wajen yaki na ruhaniya, ko a farkon mataki na shirin kafa ikilisiya ko ka yi nisa cikin tafiyar – yayen da ka ga alama ka rigaya ka kai ga wuri mai wuya da ka kasa shawo kan sa, lokaci ne na yin azumi da addu'a domin yin nasara.

5. Nemi tabbaci da jagoranci daga ikilisiyar da kake (Ayyukan Manzanni 13)
    a. Bulus da Barnaba an kiraye su, an gani an kumatabbatar da kiran su.
    b. Yin hidima a cikin ikilisiya mai lafiya zai tanadi zarafi kamar wannan domin tabbataswa da kaddamarwa.

Idan a hakin yanzu kana hidima a ikilisiya, ka mika kanka ga shugabancin ikilisiya ka kuma neman tabbataswarsu. Idan ba ka cikin ikilisiya, amma kana karatu a makarantar

koyar da Littafi Mai Tsarki ko kuma kai kadai ne mai bi (krista) cikin al'ummarku, ka nemi shawarar da kuma tabbataswa daga wasu shugabanai krista idan ya yiwu.

Tabbatar da kiran ka zai tanadi yin addu'a, tallafawa da kuma albarka yayen da an aike ka don ka kafa ikilisiya. Duk da haka, idan ka yi kokarin yi ba tare da ka nemi tabbatarwa ba, ra'ayinka za a iya gani kamar tawaye ne ko kokarin raba ikkilisiya.

6. Ka yi roko ka kuma sa ran samun salamar zuciya a matsayin tabbatar da kiran (Yohanna 14:27).
    a. Bayan tabbataswa ta hanyoyi daban-daban, ya kamata mai kafa ikilisiya ya amince ya kuma sami zaman lafiya (Filibiyawa 4:6, 7).

Ana sa sammanin cewa za a sami wasu matakai na rashin kwanciyar rai da juyayi. Duk da haka, wannan bai kamata ya zama abin da za ka ji zai hana ka shiri ba. Allah na tabbatar maka da salama bisa ga ikonsa. Daga wannan wuri ne za ka iya matsawa gaba da ƙarfin hali.

Salama da hadin kai na bukatar yin mulki a zuciyarka har ma da ta matarka idan ka yi aure. Ubangiji yana sa albarka akan hadin kai da salama, amma za a iya tabbatar maka idan matarka da iyalinka ba su da hadin kai, ba zai yiwu ba a dandana salama ta gaskiya.

7. Allah ba ya magana domin haddasa tashin hankali ko rudani. Ko a lokuttan rashin dadi, bishewar Allah za ta kawo maka salamar zuciya. (Afisawa 1:17-18; Luka 10:21)

Jagoranci daga wurin Ubangiji a kullum tana da sauki sosai. Ko da yake girman Allah yana da zurfi ya kuma fi gaban ganewa, an tabbatar mana da umurninsa yana bamu Jagorancin ta hanyar yadda zamu iya fahimta mu kuma aiwatar.

## V. DARAJA, HANGE DA KUMA SALO DOMIN IKILISIYARKA

(Kimanta Lokacin koyaswa na mintoci 45)

A. Daraja, furucin ka ne na sammani da kuma fifiko akan yadda zaka bi da aikin ka (hidimar ka). Furucin ( magan- ganun) sukan maida hankali akan battutuwan da ke a cikin hidima da suka fi muhimmanci a gare ka da kuma ikkilisiyarka.

Darajojin ka su ne abubuwa da ka gaskanta suna da muhimmanci a hanyar da ka ke rayuwa da kuma kake yin aiki. Su ne za su yi kudurta fifikon ka, kuma mai yiwuwa su ne zasu zama ma'auni da za ka yi anfani da su don shaidawa idan rayuwarka da kuma kafa ikilisiyarka ta kai matakin nasara da ka ke marmari.

Sa'ad da kai da ikilisiya ke nuna hali da ta yi daidai da kimar ku za ka gamsu. Amma yayen da wadannan ba su yi muwafaka da kimar ka ba, wato yayen da abubuwa suka tabarbare kuma da sauri zasu iya zama tushen takaici da kuma rashin jin dadi.

1. Yi addu'a domin Ubangiji ya bayyana maka kafofi (al'amura) da yake kurkusa da zuciyar sa (ya ke jin dadinsu) saboda ikilisiyarka (Zabura 127:1).
2. Ubangiji sau da yawa zai bayayyana wahayinsa (hangensa) domin ikilisiyarka bisa ga darajoji da ka ke da su tuntuni. Yi la'akari da wasu daga cikin wadannan darajoji ka kuma kudurta wadanda suka fi muhimmanci.
   - ___Bishara: dangantaka, yin wa'azi, aikin jin kai (tausayi)
   - ___Bayyananen (diddigin) koyaswa
   - ___hidimta wa kabilu da yawa
   - ___kirkirawa
   - ___fasahohi
   - ___sujada
   - ___Almajirtarwa na mutum da mutum
   - ___Hidimtawa a karamar rukuni
   - ___Sa hannu cikin sha'anin zamantakewa
   - ___Ingantaccen Hidima ga yara
   - ___membobin ikilisiya su sa hannu cikin hidima
   - ___Kafa yar ikilisiya
   - ___aikin bishara a kasar waje
   - ___Hada kai da wasu kungiyar Krista

- ___Waka da kidan al’ada masu dacewa
- ___Hikima a kungiyance (ma’aikata iri iri, ko ma’aikata da suka ba da kansu)
- ___Dangantaka ta kauna
- ___Al’ada da ya dace (daidai da al’ada)
- ___Shiga cikin all’umma
- ___Samin iko (izawa) na Ruhu Mai Tsarki
- ___Kula da membobi
- ___Hidimar da ta shafi addu’a
- ___Salo na zamani
- _____saura______________________________

Bisa ga abin da ka zaba a bisa, ko ka rubuta a madadin wadannan zabi, za ka fara ganewa wane darajoji da kuma fifiko ne zasu bayyana ikilisiyarka da kuma hidimar. A kullum darajojin suna wakiltar zuciyarka na yanzu, ko bege na gaba da burinka a matsayin shugaba.

3. Ya kamata darajojin (kimarka)  ka ta inganta hangen nesan ka. Idan ka darajanta aikin wa’azin bishara, za ka kasance da hange na kai bishara ga al’umma domin Almasihu. Idan kuma ka darajanta ikilisiyar da aka kafa, za ka bunkasa hange na ikkilisiyar cikin gida (iyali). Idan kana darajanta addu’a za ka bunkasa hange da ke jawo hidimar addu’a. Idan ka darajanta hidima ta karamar kungiya, za ka rayar da hange domin ikilisiya da za ta ribanbanya hidima.

B. Mene ne bayanin hangen nesa?

1. Takaitaccen bayani ne na makomar da kafi so don kafa ikilisiyarka a gaba.
2. Bayani ne na abin da ka ke so ikilisiyarka ta yi ta kuma zama.
3. Bayani ne na bangaskiya akan ikilisiyar Allah.
4. Yana farantawa ran  Ubangiji (Ibraniyawa 11:1, 2 da Ibraniyawa 11:6).

C. Rubuta bayanin hangen nesan ka

1. Me ka ke sa bege ga Allah ya yi maka a cikin kafa ikilisiyarka?
2. Ta ya ka dogara gare shi ya kamala ta?
3. Ka Tuna cewa bayanin hangen nesan ka ya kamata ya kasance yana nuna zuciyar kimar ka

4. Bayanin hangenka ya zama a takaice kuma takamaimai.
5. Bayanin hangenka ya zama a rubuce cikin jimloli 2-3.

D. Ka kaddamar da salon hidima domin ikilisiyarka

1. Mene ne ya zama muhimmi domin al'ada da kuma wurin da kake harin?
2. Mene ne suka fi zama bukatun al'ummar? Da farko ka yi la'akari da kimantawa na abin da kai a matsayin ka na mai kafa ikilisiya zaka bayar. Ka yi la'akari da baiwarka, basirar ka, da kuma kwarewar ka.

**Kimantawa na ciki ta na bukatar ka yi tambayoyi kamar haka:**

- Menene hali na zahiri na rayuwarka ta ruhaniya?
- Yaya al'amura A ZAHIRI suke gudana?
- Me ka ke fuskanta ka ke kuma gwagwarmaya da ita?
- Me suka zama shinge ko na kasawarka?
- Wadanne matsaloli ne masu sarkakiya ka ke fuskanta a yau?
- A ina ka ke samun ci gaba da nasara?
- Ya ya lafiyar aurenka da iyalinka ta ke?

Tambayoyin nan na iya taimakonka ka fahimci yadda ka ke yi a rayuwa da hidimarka ta yanzu. Kimantawa na ciki zai taimakeka ka kara karfi ko ka gyara wasu sassa da ke bukatar taimakon Ruhu Mai Tsarki. Idan ba tare da magance wasu al'amura na ciki kafin a kafa ikilisiya ba, za ka iya faduwa ko ka kafa ikilisiya wadda ba za ta yi aiki batun da ga farko.

Na biyu, yi la'akari da kimantawa na waje don ka kudurta matsayin na al'amura domin al'umma da kake harin za a kafa ikilisiya. Idan akwai takamaiman battutuwa, matsaloli da kuma bukatu da suka mamaye su, sai ka yi la'akari wane irin salo ko dabara za ta fi dacewa don ka hade ka kuma kawar da wadannan battutuwa.

**Kimantawa na waje ta na bukatar ka yi tambayoyi kamar haka:**

- Menene ainihin hali na al'adarku?

- Me ya ke faruwa a cikin al'ummarku da ya shafi ikilisiyarku?
- Me yake faruwa a ikilisiyarku da ya shafi al'adarku?
- Menene matsaloli da mutane ke fuskanta?
- Menene ke wakana?
- Yaya zai kasance idan samaniya ta mamaye al'ummarku ta wurin ikilisiyarku?

Tambayoyin nan na iya taimakonka ka fahimci yadda al'ummarku ke aiki, da kuma wadanne bukatu suka mamaye wurin. Zai taimakeka ka kirkiro gada na kai bishara/ alaka da ta dace don biyan bukatun mutanen.
Ka Gina gadar dangantaka daga wurin ka da kuma ikilisiyar da aka kafa wa al'umma. (I Kor. 9:19-23).

Gadar dangantaka ita ce mahadin zuwa zukata da kuma ran al'ummar da kake hari. Ita ce wuri tushi da zata ba ka damar haduwa, sadarwa da yi Masu hidima.

***Dauki mintoci 20-30 domin ba dalibai damar rubuta bayanin hangen su. Ka ba dalibai da yawa damar don su shaida a fili bayanin hangensu.***
*Wannan lokaci ne mai kyau don a bada horaswa da kuma jagoranci idan dalibai sun yi kuskuren fahimtar aikin da aka ba su.*

**Ku Kammala wannan sashen da bayanan ƙarshe da zasu biyo a kasa.**
(Lokacin koyaswa mintoci 15)
E. Raba, yi bita da sake tacewa da wasu domin bada lissafi da kuma tallafawa.
1. A matsayin ka na shugaba yana da muhimmanci ka shaida darajojin ka, hangen ka, da kuma salon hidimar ka da wasu shugabanai ko shugabannai masu anfani a gaba.
2. Tare za ku iya bitar kowane kashi kuma kuyi la'akari da manufarsu kuma kuyi addu'a don ci gaba da bayyanawa da da bayyana rawar da suke takawa a cikin aikin.

3. Tsaftace dabi'un ka, hangen ka da salon ka bayan samun ra'ayi daga amintaccen shawara.
   a. Samun hikima daga kwararun shugabannai zasu iya taimakon ka ka ceci (adana) lokaci, kuzari da kuma al'bakarkatu.
   b. Tattaunawa tare da wasu shugabannai na iya tabbatarwa da taimakawa wajen fahimtar alka'lumma da kuma al'umma da kake hari.
   c. Shawara na gari za ta taimakeka ka maida hankali a kan abubuwa da suke da muhimmanci ka kuma jinkirta abubuwa da suke na gaba.
   d. Idan sauyi ya zama dole, ka daidaita dabi'un ka, hange nesan ka da kuma salon da za ka yi anfani da su cikin kafa ikilisiyarka.

VI. **SHIRI DA TSARI**
(Lokacin koyaswa mintoci 45)

A. Shiri da saka Makasudi (buri) aiki ne na ibada

Yin shiri da kuma saka Buri aiki ne na fahimta da aiwatarda makakai don daidaita ka, hangenka zuwa ga shirin Allah da manufar sa. Misalai 29:18 ya bayyana cewa idan ba tare da hange ba, mutane za su halaka.

1. Kalmar nan hange na nufin, wahayi daga wurin Allah game da shirinsa.
2. Kalmar nan hallaka na nufin, zama ba linzami, rashin alkibla ko maida hankali.
   a. Allah ya yi shiri domin dukan halitta (Ishaya 37:26).
   b. Allah ya yi tsare-tsare domin kowane mutum. (Irmiya 29:11).
   c. An nuna Tsarin dabaru a nassi da dama a cikin Littafi Mai Tsarki.
      - Jethro ya umarce Musa don ya yi dabarar wakilci. (Fitowa 18:1-27)
      - Allah ya umarce joshua ta yadda zai ci Jericho da yaki (Joshua 6)
      - Nehemiah ya tsara ya kuma aiwatar da tsari na sake gina ganuwar Urushalima (Nehemiah)
      - Yesu ya tsara shiri don daukar almajirai, horas wa da kuma aika su domin shelar Bishara (Ayyukan Manzanni 1:8)
      - Bulus yana da shiri don ya yi wa'azi inda babu mutum da ya yi. (Romawa 15:20).

B. Mutane da yawa suna da hangen nesa amma mutane kadan ne suka kirkirir dabarun da zasu iya su aiwatar. Dole ne mai kafa ikilisiya ya nemi nufin Allah kuma ya dauki lokaci da yin kokari don kirkirar Tsarin da ya dace. (Yakubu 4:15, 15).

1. Yi la'akari da rayuwar Yusufu da yadda Allah ya ba shi mastayi ko a cikin shan wuya da kuma gwaje-gwaje don ya koyi gudanarwa, tsari da kuma shiryawa.
2. Yusufu ya koyi yadda zai gudanar da al'amura da za su ba shi damar lura da iyalinsa da dukan duniya a lokacin yunwa mai girma a shekarun.
3. Hanyar yin tsari ta na ba wa Ubangiji dama ya aikata al'ajibai na tanadi da kuma albarka.

C. Dole ne Dabarar ta zama a bayyane, a rubutacce da kuma aunanu.

1. Tsari dole ta zama a fili bayyananen aiki abubuwa za a yi.
2. Kowane abu ko dawainiya ya kamata ya sami sakamako da ake so.
3. Kowane sakamako zai iya zama aunanne ko a lamba ko a lokaci.
4. wadannan abubuwan na bukata a saka su a cikin kalanda domin a yi bin diddigi don samun ci gaba.

5. Kammalalun abubuwa da kuma adadi ya kamata a yi murnarsu yayen da kowace mataki na dabarar an kammala shi.
6. Sakamako ba daya bane da mafita ba.
    a. Sakamako: abin da ya faru a dalilin aiwatarwa ko tsari.
    b. Mafita: adadin wani abu da aka fitar ta wurin wani mutum ko wani abu.
    c. Sakamako: suna canzawa, canjin tasiri, kuma ana iya gani ta hanyoyi daban- daban. Mafita: Abin da ana aunawa bisa ga yawa kuma za a iya shar'antawa kadai bisa ga yawan ba a ingancin ba.
    d. Sakamako bisa ga niyya zai kai ga lafiya, sauyawa da girma a yawan lamba.
    e. Kiddigar tushen sakamako zata ba da bayanai don karfafa raunin da kuma magance wuraren rashin.

D. Yin tsari da dabara na taimakawa wajen fadada fa'idar ka (kokarin) ka (Misalai 29:18).

1. Shugabanai nagari suna yin tsare-tsare su kuma aiwatar da su. Misalai 16:3, Zabura 90:12)
2. Ruhu Mai Tsarki zai jagorance ka wajen yin tsarin (Zabura 20:4, Zabura 16:9, Ishaya 28:29).
3. Anfanin ka a gaba za ta karu sa'adda sha'awarka ta hadu da shirin Allah.
4. Kammala aiki da kuma ganin ci gaban ka zai kara kuzarinka da wahayi don nasara a cika shiri da kuma dabaru da aka tsara.
5. Anfani na gaba tana karuwa sosai sa'ad da kuka yi aiki tare (hada kai) da kungiya saboda dalilin cika hangen nesan!

## VII. GWAMNATIN IKILISIYA DA SHUGABANCI

(Lokacin koyaswa mintoci 45)

A cikin Littafi Mai Tsarki, an kwatanta ikilisiya ta hanyoyi da yawa. Mun lura cewa ikilisiya rayayyiyar talika ce, nunin jikin Kristi. Mun kuma san cewa ikilisiya kungiya ce wanda Kristi ya kafa da ta wurin jagoranci da kuma umurni da aka zayyana cikin Littafi Mai Tsarki. A matsayin kungiya wanda Ruhu ke bishe ta, Allah ya kafa shugabanci domin iza girma, yin bishara, zumunta da kuma lafiya. A duk cikin tarihi, tushen tsari guda uku na gwamnatin ikilisiya sun mamaye shugabancin krista. Wadannan tsarin kada a rudar da su da dariku ko halaka da ita, amma nuni ne na tsari wanda ke cikin makasudin mua'mular majami'u na gida.

**Za mu tattauna wadannan tushen tsari guda uku na gwamnatin sa'an nan za mu dubi abin da muka samu a cikin Nassin Littafi Mai Tsarki**

A. Shugabancin Ikilisiya kadai

Ikilisiya ta sha yin koyi da tsarin siyasa na al'adun yankinsu tare da karfi da lahani. Tabacen rubuce-rubuce na ubannin (iyayen) ikilisiya, shugabancin ikilisiya kadai ta yi alaka da shugabancin Daular Romawa. Kamar yadda sarki ya kasance mafi girma akan Jiki, bishop, dattijo haka ma fasto ya ke da iko bisa al'amuran ruhaniya, yana shugabantar dukan dikinoni da membobi. Ikilisiyoyi masu zaman kansu suna da yawa ayau masamman a dukan fadin ikilisiyar darikar Roman Katolika. Duk da yake wannan tsari na gwamnati ta tabbatar da inganci, cin hanci da rashawa ita ce hadarin a kullum.

B. Shugabancin Ikilisiya Na Taron Jama'a

Bisa ga karfafawa da a ke yi kowane mai bi firist ne, gwanatin ikilisiya ta mamaye ikilisiyar Protestant, Irin tsarin gwamnatin ikilisiya nan samun ta ne a ikilisiyoyin Baptist, ya zamana tana da shugabannai haka dattawa, fastoci, dikinoni da kwamitin amintattu. Amma, ikon yana ga membobin taron jama'a. membobin ikilisiya suna iya yin zabe dangane da kasafin kudi na shekara-shekara, shirye-shirye na ikilisiya da kuma matsayi na shugabanci. Bambance bambance sakamakon tsarin nan zai iya zama marar kyau, amma karin da ba da lissafi na iya hana cin hanci da rashawa.

C. Shugabancin Ikilisiya Na Dattijai

Wata tsari sananniya ita ce ta shugabancin gwamnatin ikilisiya na Dattijai. Wannan a saukake na nufin cewa Dattijai ne ke shugabanci Ikilisiyar. kilisiyar, wanda dikinoni ke goyon baya. Taron jama'ar ikilisiya suna da karancin yin Magana a yanke babban shawara na ikilisiya, amma wadanda suke da cancantar ingancin Littafi Mai Tsarki domin yin shugabanci suna raba nauyinn ikon. Ko da yake wannan tsari na iya Habaka Hali na "su da mu" tsakanin ikilisiya da dattawa, yana haifar da matakin daidaito na yi da kyau da kuma ba da lissafi.

Lura da ire iren tsari na Gwamnatin Ikilisiya ta ba mu zarafin yin la'akari da addu'a yadda ya kamata mu kafa shugabanci don sabuwar ikilisiya da aka kafa.

**Aikin yi a Rukuni**: *Dauki lokaci a kuma lura wadanne irin tsari (sigogi) na gwamnatin ikilisiya ka kasance ciki a baya. Rubuta abubuwa kadan masu kyau da ka tuna game da wannan salon mulki.. Yanzu ka rubuta abubuwa kadan wadanda ka tuna da za a iya gani ba za su zama lafiyayyu ko bisa ga Littafi Mai Tsarki ba.*

D. Dalilai muhimmai guda uku da su ka sa ana bukatar Gwamnatin Ikilisiya.

- Zai kawo kamantuwa bisa ga Littafi Mai Tsarki mafi girma.
- Zai daukaka ruhaniya da kuma hadin kan kungiya mai girma.
- Zai tabbatar da bada bayani da lissafi mafi girma na shugabanci.

**Sa'ad da a ke duban wata tsari na musamman na gwamnatin ikilisiya, ya kamata a yi kwakwaran tambayoyi:**

- Aikatacciya ce?
- Ta gargajiya ce?
- Ta tarihi ce?
- Abin dogara ne?
- Shin al'ada ta na iya fahimtar ta?
- Mafi mahimmanci duka, **<u>Ta na bisa tafarkin Littafi Mai Tsarki</u>**?

Ya kamata muyi iya kokarinmu don daidaita tsarin gwamnatin ikilisiyarmu da abin da muka luru da shi a cikin ikilisiyar Sabon Alkawari. Ko da yake wannan a kullum ba mai yiwuwa ba ne bisa ga wurin da mu ke ko iyakar mu, tsarin gwamnatin ikilisiya ya kamata ta yi aiki bisa salon Littafi Mai Tsarki da kuma gaskiya kamar yadda a ka nuna ta wurin rayuwa da kuma koyarwan Yesu, manzanni da kuma ikilisiyar Sabon Alkawari.

E. Sarauta (lakabi), aiki da kuma matsayi (mukami) na shugabannai masu mulki

**Dattawa**

Kalmar da aka fi sani a cikin fassarar Littafi Mai Tsarki na Turanci da ke nufin wadanda Allah ya zaba don tanadar da shugabanci ga ikilisiya shi ne "dattijo". Wani lokaci ana amfani da kalmar "mai lura" tare da dattijo. A bayyane yake daga I Tim. 4:11-5:2, cewa za a nada dattawa don aikinsu bisa ga cancanta. Zaben ya ga bisa nuna baiwa ta ruhaniya, balaga, fahimta, dabi'a, da kuma tasiri.

A cikin Sabon Alkawari, dattawan ikilisiya suna da alhakin kowane fanni na rayuwar ikilisiya yayin da suke wa'azi, koyarwa, gudanarwa, ba da shawara, kiwatarwa (kiwo), yin annabci, kwabaswa( yin gyara), jagoranci, tsawatarwa, horo, gudanarwa. Bugu da kari, bisa ga Ayyukan Manzanni 4:36-37 da Ayyukan Manzanni 11:29-30, dattawa suna kula da kudaden Ikkilisiya, Kuma suna yin taka tsantsan don kauce wa duk wani abun da bai kamata ba.

*Bisa ga Littafi Mai Tsarki Babban Fasto ya kamata ya zama dattijo mai jagorantarwa a sakanin jama'ar ikkilisiya.*

**Dikinoni**

Wani nau'in jagoranci na ruhaniya a cikin Sabon Alkawari shi ne, "dikon". Kalmar na nufin, "bawa". Sa'ad da akayi amfani da ga wani nau'in mai hidima na Ikkilisiya, yana kwatanta maza da mata wadanda suka sami izini daga dattawan ikilisiya don su iya yin hidima ta musamman ta hanyoyi daban-daban. Hidimar dikin baiwa ce da Manzo Bulus ya bambanta daga duk dattawan ikilisiya da kuma taron jama'a (Filibiyawa 1:1).

**Manzanni**

Kalmar da aka yi amfani da ita don kwatanta wasu, amma ba duka ba, shugabannai na ruhaniya a cikin Sabon Alkawari, ita ce kalmar, "manzo". Wasu lokuta an yi amfani da ita don bayyana wadanda a ka san su guda Sha Biyu wadanda suka yi tafiya tare da Yesu a lokacin rayuwarsa a duniya, amma a yanayi (mahallin) shugabancin ikilisiya an fi danganwa da irin dattijo na masamman. Hanya daya na bambantawa tsakanin manzanni da kuma yawancin fastoci ita ce yawancin fastoci dattibai ne wadanda suke hidima ga wata majami'a ta musamman sa'an nan manzanni dattibai ne da suke hidimtawa a wuri mafi fadi na yanki, kasa, ko dukan Jikin Kristi a ko'ina.

Kafa Majalisar Manzanni Masu Lura ta apostolic a waje ta kunshi kwararrun shugabanin ikkilisiya masu hikima kuma wadanda hidimarsu da kuma shaida a kansu ta je da nisa fiye da cikin taron jama'ar ikilisiyar. Aikinsu shi ne su bada kula ta ruhaniya ga ikilisiya; su ba da shawara ga shugabanci dangane da al'amura na hidima da na kuma gudanar da mulkin, su kuma shiga cikin zaben Babban Fasto yayen da ofinshin ya zama babu kowa. An ba su matsayin don shiga cikin horo na Babban Fasto a duk lokacin da ya wajaba, har ma su sasanta rikice-rikice na ikilisiya da ba a iya sasantawa ta hanyar al'ada ba.

A kullum Majalisa ta waje ta Manzanni Masu Lura daya ne da rukunin mutane da suka taimaka wajen aikar (tura) da mai kafa ikilisiya a kuma kafa ikkiliya, ko da yake ba koyaushe haka lamarin yake ba.

**Ikilisiyoyin Manzanni**

Wasu ikilisiyoyi wasu lokuta suna da shafewa (kebewa) a kan su wanda ta zarce mizanin taruwar masu bi guda daya, ko saboda sun kafa wasu ikilisiyoyi da dama ko saboda shahararsu da tasirinsu a kan shugabanni na wasu ikilisiyoyi da yawa. Irin wadanan ikilisiyoyi ana Kiran su "ikilisiyoyi manzanni". Kada a rikita shi da darika ko rukunai, amma sai dai aikin da kuma tasirin wannan musamman. Babban Fasto na irin wannan Ikkilisiya yawanci yana aiki ba a matsayin shugaban ikilisiyar wurin kadai ba (Ikilisiyar gida), amma kuma a matsayin manzo a cikin wasu yankuna na Jikin Kristi gaba daya.

Har ila yau Ikilisiyoyi wasu lokuta suna da shafewa (kebewa) a kansu wanda ta zarce mizanin taruwar Ikkilisiya guda na masu bi, ko saboda sun kafa ikilisiyoyi da dama ko kuma saboda shahararsu da kuma tasirinsu a kan shugabanni na ikilisiyoyi da dama. Irin wannan ikilisiyoyi ana kiran su "ikilisiyoyin Manzanni", ta wajen amfani da Kalmar ta bambanta daga kowace manuni zuwa ga takamaiman kawar da shakka na rukunai dangane da Allah Uku cikin Daya. Babban Fasto na irin wannan majami'a baya aiki a matsayin faston ikilisiya guda ta gida kadai ba, amma kuma a matsayin manzo a cikin yanki na fadin Jikin Kristi.

F. Gwamnatin Ikilisiya na da Mahimmanci domin shugabancin bada lissafi.

Bayyananiya da kuma gwamnatin ikilisiya mai amfani tana da muhimmanci don karawa da kuma karfafa bada lissafi ga dukan shugabanci ciki har da Babban Fasto. Kasancewa

da karfi, bayyananen tsari na bada lissafi a wurin yana da matukar muhimmanci. Idan ba tare da bayyananiyar gwamnatin ikilisiya ba, ikilisiyar zata fuskanci rashin aiki da kuma rashin kamewa. Tsarukan da aka kafa ya kamata su goyi bayan faston Duk da haka ya samar da Yanayi na lafiya da rikon amana. Bada lissafi ba nuna iko ba ne, amma domin kirkiro tsaro don a tabbatar da lafiyar dabi'a, ruhaniya da kuma lafiyar kudin ikilisiya.

G. Ruhaniya Mafi Girma da kuma hadin kan Kungiya

Ikilisiya za ta gano ta kuma amfana daga shugabanci na Littafi Mai Tsarki ta wurin dattawa. Majalisar dubawa na manzanni, da kuma dikinoni. kowane a wurin nasa aikin da kuma gudanar da hidimar ikilisiya don cika manufarta. Ikilisiyar da ke da hadin kai tana da ƙarfi sosai, duk da haka ikilisiya wadda ba ta da hadin kai (dayantuwa) cikin ruhu da kuma a kungiyance a karshe za ta fadi (Markus 3:25).

An kwatanta Shugabanci na Littafi Mai Tsarki ta hanyoyi da yawa daban-daban a cikin Nassi. Daya daga cikin hallaye da aka fi gani shine hadin Kai. Afisawa 4:11-16 ya ba da wani tabbaci Sarai cewa ikilisiya a matsayin cibiyar shiryarwa tana da hadin kai (dayantaka) a tushen mai da hankalin ta, kuma hadin kai
yana da muhimmanci ga fadada Mulkin Allah.

**Mahimman ra'ayoyi dangane da aiki da gudanar da matsayi**

- Dattawa suna aiki tare kuma tare suke yanke shawara.
- Ikon ruhaniya a kullum ana bada wakilci, ba'a taba dauka ko a yi zabi a Kai ba. Saboda haka ake nada Dattawa.
- An kirkiro dikinoni saboda tunkarar bukatu.
  Dikinoni ba su yin mulki, amma suna hidimtawa ne. Watakila Ba za a bukaci dikinoni ba har sai ikilisiya ta yi girma (bunkasa).
- Dattawa daidaiku suna da iko kadan, amma a gabadaya (a tare) suna da iko mai girma.

**Kada a tsara gwamnatin ikilisiyarku ya wuce misali**. Bisa ga mahallin ku gwamnatin ikilisiya na iya zama mai sauki. Duk da haka, idan Ubangiji ya bar ikilisiyarku ta yi girma ta yi yawan mutane da kuma tasiri, kada ayi watsi da gwamantin da kuma tsarin. Sakaici

da gwamnatin ikilisiya zai hana ikilisiya girma cikin yanayi na koshin lafiya. Ko a cikin ikilisyoyin gida da kuma ikkilisiyu na karkara, ana bukatar Shugabancin gwamnati.

## VII. KUNGIYAR KAFA IKILISIYA

(Lokacin koyaswa mintoci 60)

A. Allah ya na amfani da kungiyoyi don cika nufinsa. (2 Timoti 2:2).

1. Uku cikin Daya misali ne na kungiya.
2. Yesu ya kwarara rayuwarsa a cikin mutane goma sha biyu na tsawon shekaru uku
3. Yesu ya aiki kungiyar mutum biyu-biyu (Luka 10:1, Markus 6:7).
4. Kungiya tsari (salo) ne na Littafi Mai Tsarki (Ayyukan Manzanni 13:2)
5. Aure misali ne na kungiya da Allah ya tsara (shirya).
6. Dan kungiyar ka na farko shi ne kuma ya kamata ya zama matarka ko mijinki.
    a. Ya kamata matta da mijji su kasance cikin hadin Kai kafin su yi yunkurin kafa ikilisiya.
    b. Allah ya kira magidanta su zama shugabanin ruhaniya na iyalansu. Lafiyar ruhaniyar iyalinka alhakin ka ne (nawayarka). Mazaje su nuna kauna mai sadaukarwa ga matayensu karmar yadda Christi ya nuna wa amaryarsa, wato ikilisiya (Afisawa 5:25).
    c. Banda dangantakar ka da Allah, dangantakar ka da matarka ita ce mafi mahaimmanci. Allah yana son mazaje su kaunaci matayensu su kuma ba da kansu ga girman ruhaniyar matayensu. (Afisawa 5:25-27).
    d. Akwai matakai da za ka iya dauka a kowace rana da za su taimaki aurenka ta girma. Kowace rana zarafi ne don ka sa aurenka ta yi kyau ko ta yi muni (lalace). Kamar yadda mai gona ke ba da hankali a gonarsa babu fasawa, kai ma ya kamata ka ci gaba da inganta (gyara) aurenka. Wadannan ayyuka hudu masu sauki za su taimaka sosai wajen karfafa aurenka.
        - Kowace rana, ku yi addu'a tare.
        - Kowace rana, ka fada wa matarka kana kaunarta.
        - Kowace rana, ka yi wani abu don taimakon ta
        - Kowace rana, ka gode/yaba mata da gaskiya.

B. Aiki cikin Kungiya ya fi tasiri fiye da aiki kai kadai.

1. Bambancin kyaututtuka da kwarewa na wakilce a cikin kungiya. (I Korantiyawa 12:4, 2 Timoti 4:11).

2. Kungiyoyi suna tallafawa (bada taimako) a lokacin wahala da kuma gwagwarmaya (Mai Wa'azi 4:10).
    a. Doki daya zai iya daukan kaya mai nauyin ton biyu.
    b. Domin haka, dawakai biyu zasu iya jan ton hudu.
    c. Amma idan an yi musu karkiya su biyu za su iya jan ton goma sha tara.
3. Ka roki Allah ka kuma nemi gina tawagar hidima mai ninki biyar.
    a. Baiwar (kyaututtuka) hidima suna nuna tsarin Allah. Su siffa ce ta cikakken ofishi ko kira, maimakon baiwar da za ta iya aiki a ciki da ta wurin kowane mai bi. Idan an dubi Afisawa 4:11-13 ta nuna cewa ba dukan masu bin Yesu su ke da baiwar hidima ninki 5 ba. Littafi Mai Tsarki ya ce a filli "wasu".
    b. Misali: Saboda wani ya yi annabci, bai nuna cewa mutumin annabi ne ba. Haka ma, akwai wadanda da suke da mukamin Fastoci wadanda ba su da baiwar fastoci, amma suna iya kasancewa da baiwar izawa na mulki /shugabanci.
    c. Ya kamata baiwa ta ba da hanya ga sarauta (suna). Kada ka zagaya kana ta shaida kanka a matsayin 'Annabi X" ne ko 'manzo X'. Idan kai manzo ne ko annabi, ko kai an ba ka wata baiwa ta hidima wadansu za su ga baiwar a cikin ka za su kuma san ka da kuma baiwar.
    d. Wannan amincewa ba koyaushe yake haɗe da SUNA na ofishin hidima ko kyauta ba. Mutanen da suke shela da sanar da kansu suna iya ko ba za su kasance masu gaskiya ga iƙirarinsu ba. Cin zarafin wannan 'ofishin' ko kyauta ya haifar da damuwa sosai na tsawon shekaru.

**Bangarori 5 na Hidimar kungiya (baye-baye) ana iya gabatar da su ta gwadawa da hannu**

- **Manzo** – Manzo yana kafawa da kuma gina ikilisiyoyi, shi mai kafa ikilisiya ne. Manzo yana iya yin aiki da yawanci ko dukkan baye-baye na hidima. shi ne "babban dan yatsa", mafi karfi duka a cikin yatsun hannu yana iya taba kowace yatsa.

- **Annabi** – Annabi a harshen Hallenanci na nufin “fadar abin da zai faru” wato yin furci a madadin wani. Annabi mai Magana ne da yawun Allah, yana furta Maganar Allah. Annabi shi ne “yatsa na kusa da babban yatsa” ko yatsa da ke yin nuni. Yana nuna abin da zai faru nan gaba da kuma nuna zunubi.
- **Mai Wa’azin Bishara** – Mai Wa’azin bishara ana kiransa da mai shaida ga Yesu Kristi. Yana aiki domin ikilisiya don kawo mutane zuwa cikin jikin Kristi inda za a almajirtar da su. Yana iya almajirtarwa ta wajen waka, kwaikwayo, wa’azi, da kuma wasu kirkirarun hanyoyi. Shi ne “yatsa ta tsakiya”, mafi tsawo duka wanda za a iya hanga a cikin taron mutane. Masu wa’azin bishara suna jawo hankula da yawa, amma an kira su ne domin su hidimta wa jikin Kristi a wurin.
- **Fasto** – Fasto makiyayi ne na jama’a. Makiyayi na gaskiya yana ba da ransa domin tumaki. Fasto shi ne ‘yatsar sa zobe”. Ikilisiya ta aure shi; an kira shi don ya zauna a wurin, ya lura(reno), ya ciyar sa’annan ya jagorantar.
- **Malami** – Mai koyarwa (malami) da kuma fasto a kullayomi suna tarayya da ofishi amma ba kullum ba. Malami yana sa harsashi kuma yana sa hankali kan abin da yake dalla dalla kuma yake daidai. Yana murna cikin yin bincike don tabbatar da gaskiya. Mai koyarwa shi ne “karamar yatsa”. Ko da yake ana ganin karami ne kuma ba a ganin muhimmancinsa, an tsara shi musamman don tonowa da zurfi cikin matsatsiyar wuri da kuma wurare masu duhu, yana haskakawa da tattara Maganar gaskiya.

Yayen da ba zai yiwu a sami wakilcin dukan kyaututtukan 5 na hidima a cikin kungiyarku ba, mai kafa ikilisiya ya wajaba ya tabbatar cewa kungiyar sa na da kyaututtuka dabam-dabam don zama da tabbacin cewa kungiyar ta kasance da Karin amfani kuma za ta iya kai wa ga kowane irin mutum.

C. Horas da Kungiya ya fi daukan ma'aikata. Horaswa almajirtarwa ne.

**1.** Cusa hangen nesa na shuka Ikilisiya a cikin membobin ƙungiyar ku don su iya rungumar hangen nesan da tsari.

a) Hangen nesan ya kamata ya zama bayyane, Sauƙin ganewa, a takaice da kuma mai Tursasawa

1. A bayyane: ya kamata hangen nesan ta zama a rubuce kuma a bayyanar da ita ga fahimtar kowa ta hanyar da ba za a sami tambayoyi game da hangen ba.
2. Sauƙin ganewa: Hangen na bukatar zama sahihi mara duhu domin mutane su sa hannu ayi aiki tare.

3. Takaitacce: Hangen na bukatar a takaitashi yadda kungiyarku za ta iya fahimta a saukake su kuma jawo hankalin wasu.
4. Mai tursasawa: hangen nesa yana bukatar ya zama mai tursasawa da iya kwadaitar da membobin kungiyar, da kuma membobin Ikilisiya na gaba.

2. Cusa dabi'u na kafa Ikilisiya a cikin membobin ƙungiyar ku.

a. Kimar mai kafa Ikilisiya da ƙungiyar ya kamata su kasance dai-dai.
   1. Daidaitattun dabi'u suna kawo haɗin kai ga ƙungiyar.
   2. Daidaitattun dabi'u suna ba ƙungiyar damar magance matsaloli tare ba tare da rarrabuwa ba.
   3. Daidaitattun dabi'u suna kawo kwanciyar hankali idan matsala ta taso, ko kuma an yi zargi.

b. Ka Koyas game da dabi'u waɗanda ke ayyana aikinka da tafiyar ka tare da Ubangiji, da kuma ƙimar da ke ayyana kafa Ikilisiyar ku.
   1. Ka yi nuni da kuma aiwatar da dabi'un a cikin gidan ka.
   2. Ka nuna da kuma aiwatar da dabi'u a cikin jama'a.
   3. Ka taka rawa muhimma a cikin ƙungiyar ku don su yi koyi da aiwatar da waɗannan dabi'u a rayuwarsu ta yau da kullun

3. Almajirtarwa na bukatar lokaci da kuzari.

a. Almajirtarwa ba shiri ba ne amma tsari ne na girma ta hanyar dangantaka.
b. Yesu ya bada dukan lokacinsa, karfinsa da kuma kokarinsa a cikin mutane goma sha biyun na tsawon shekaru uku.
c. Wasu mutane za su yi girma da sauri sosai fiye da wasu. Wasu mutane za su girma sosai fiye da sauran. Dukan mutane na bukatar lokaci da karfi don a almajirtar da su.
d. Kankantar lokaci da aka sa wajen almajirtarwa da horar da ƙungiyar ku, zai haifar da sakamako mara kyau.

e. Ka jagorantar da mutane zuwa ga wurin balaga (girma) ta ruhaniya domin su iya fara taimakon wasu ta salo kamar haka.
f. Ka Gano hazaka, basira da ilimin mutane.  Taimaka wa mutane sanin ainihin abin da suka ƙware a kai, sannan ka sanya su su yi hidima a wannan matsayi.
g. Ka maida hankali a kan karfin mutane, sa'annan ka taimake su su girma su kuma ci nasara da karfinsu.

h. Ka Magance matsalolin hali a cikin tsarin almajirantarwa. Mutane masu fasaha, ilimi da mutuntaka waɗanda ba su da mutunci za su ƙare cikin gazawar ɗabi'a.
i. Kasancewa da mutanen da suka dace a wuraren da suka dace yana da mahimmanci don gina ƙungiya. Canje-canje masu ƙarfi na ƙungiya na faruwa bisa ga jeri na mutane. Yi Duba akan waɗannan bayanai daga Dr. John Maxwell akan ginin ƙungiya da sanyawa inda ya kamata.

- Mutum wanda bai Dace ba a matsayin Da Bai zama dole Ba = Koma baya, za ku lalace
- Mutum wanda bai Dace ba a matsayin Da ya zama Dole = Takaici, za ku sha kunya
- Mutumin Da Ya Dace a Matsayin Da bai Dace = Rudewa, ba za su san dalilin da ya sa suke hidimtawa a nan ba.
- Mutum Da Ya Dace A Matsayin Da ya Kamata = Ci gaba, za ka ci gaba da nasara.
- Mutane Da Suka Dace A Matsayin Da Suka Dace = Ninkawa, za ku sami ƙarfi da yawa.

IX. **YAKI NA RUHANIYA DA KUMA KAI BISHARA**

(Lokacin koyaswa mintoci 45)

A. Yaki na ruhaniya zai faru (Afisawa 6:12)

1. Magabci zai yi tsayayya da himmar jama'ar Allah da kuma shirinsa. (Markus 3;27).
2. Yakin ruhaniya zai faru a fagen fama da yawa.
   a. A rayuwarka (Yakubu 4:7)
      1. Mun yi nasara da magabci ta wurin jinin Dan Rago da kuma shaidar bakin mu. (Ruya ta Yohanna 12:11)
      2. Ta wurin matsayin iko a cikin Kristi (Afisawa 1:20-21, 2:6, Kolosiyawa 2:13-15, Luka 10:17, Matta 28:18).
      3. Ta wurin garkuwar bangaskiya da kuma takobi na Ruhu (Afisawa 6:16, I Bitrus 5:9, Matta 4:4, 7:10).
      4. Ta wurin mallaka tunani da kuma kawo su karkashin ikon mu (Romawa 12;2).
   b. A cikin matakai daban- daban na ikoki da kuma mazauna daban-daban
      1. Jibrailu ya bukaci taimakon Mika'ilu domin yin nasara da sarkin Persia. (Daniel 10:11-21)
      2. Akwai wuraren zaman ikokin ruhohi daga yanki, zuwa birni/kauye zuwa ga daidaiku. Suna bukatar a magance su ta hanyar da ta dace (Afisawa 6).
      3. Yi addu'a cewa Allah ya ba ku fahimta ta ruhaniya don gani da gane mutum mai ƙarfi mai mulki.(2 Korantiiyawa 10:4)

B. A gano wuri ko wuraren kai bishara. (Luka 10:8)

1. Wuraren da babu ikilisiyoyi.
2. Wuraren da suke da tasirin dabaru.
3. Wuraren da za su yi tasiri sosai ga al'ummar ko birni gaba daya.

C. Nemi wurare da ke da matukar bukata.

1. Wuraren da ke da tsananin talauci.
2. Wuraren da ke da rashin aiki (karancin anfani).
3. Wuraren da ke da marasa lafiya da yawa, marasa galihu da waɗanda aka manta da su.
4. Wuraren da suke da duhu na ruhaniya.

5. Wuraren da ba a dauke su kome ba saboda ana ganin kamar ba su da bukata.
    a. Al'ummomin masu arziki
    b. Al'ummomin masu hannu da shuni
    c. Wurare da ke da 'yan siyasa ko jami'an gwamnati.

D. Da farko ka tafi ka kai bishara ga wadanda ba su ji ba. (Romawa 15:20)
1. Yesu ya zo domin nema da kuma ceton battatu
2. Bulus ya bayyana sarrai, burinsa ita ce ya tafi inda ba wanda ya taba yin wa'azin bishara a wurin.
3. Ka tafi inda akwai girbi na batattun mutane da ke a shirye don a kai musu bishara.

E. Daga nan har zuwa iyakar duniya. (Ayyukan Manzanni 1:8).

F. Ka yi Azumi da Addu'oin zagaye na wurin da aka gano. (Joshua 1:3).
1. Yi addu'an gaba da mazaunin ruhohi.
2. Yi addu'a domin albarka a kan mutanen
3. Yi addu'a domin Ubangiji ya bayyana budadden zukata domin Bishara (Matta 10:11-13, Luka 10:5-9).

G. Ka yi bishara ga marasa bin Yesu a wurin da a ka gano.
1. Kai da kungiyarka ku shaida kaunar Kristi
2. Ka tunkari mutane cikin kauna da tausayi, kada ku yanke hukunchi akan su.
3. Ka Ba da shaidarka da kuma aikin fansar Allah a rayuwarku. (Romawa 15:18).
4. Bayyana wanene kai (yadda kake) kafin ka sadu da Kristi, da kuma wanene kai a yanzu tare da Kristi.
5. Nuna yadda Kristi zai iya kawo bege, kauna, karbuwa da kuma fansa a gare su suma.

H. Yi addu'a domin mutane. (Yohanna 14:12, Matta 10;8)
1. Yi addu'a domin marasa lafiya su sami warkaswa.
2. Yi addu'a domin wadanda ake tursasawa domin su tsira.

I. Ka bayyana Bishara dalla dalla.
1. Yesu Kristi shi ne hanya kadai. (Yohanna 14:6).

2. Yi addu’a tare da batattu cikin tuba, furta Yesu Ubangiji ne da kuma ba da kai ga bautarsa.

J. Ka shigar da mutane a hanya mai ma'ana wadda ta wuce iyaka da wa’azin bishara.

1. Gayyaci mutane zuwa ikkilisiya
2. Gayyace su zuwa dangantaka da ke ci gaba.
3. Mutane suna neman ingantaciyar alaka, ba kawai tallace tallace ba.
4. Ka Ba wa sabon tuba Littafi Mai Tsarki in ya yiwu.
5. Ka bayyana musu mataki na gaba cikin bangaskiyarsu, ka kuma taimake su su shiga cikin matakin almajirci.
6. Karfafa sababbin tuba su fada ma wasu game da bangaskiyarsu cikin Kristi. (Romawa 1:16)

## X. KA HADA SABABBIN TUBA DA HANYAR ALMAJIRTARWA

(Lokacin koyaswar mintoci 60)

A. Kungiyar kafa ikilisiya a yanzu tana almajirtar da sababbin Krista bisa ga gwanin su na almajirtarwa da suka koya daga fasto mai kafa ikilisiya.

B. Idan kungiyar mutum daya ne ko mutane biyu, daga nan wadannan sababban almajiran za su zama "kungiyarka" na farko yayen da suka shiga matakin almajirtarwa.

C. A lokacin matakin almajirtarwa, ka sa sababbin tuban su aiwatarda da abin da suka koya.

1. Zama Misali, yin nuni da kuma aiwatar da abin da aka koyar (Matta 4:19).

***Misali: Wa'azin Bishara***

a. Ka nuna musu yayin da suke kallo.
b. Ka yi tare da su domin su sami kwarewa.
c. Ka ba su izini don su yi, sanan kayi duba kana lura da kuma taimakon su.
d. Ka bar su, su yi da kansu.

2. Ka Koyar ta hanyar amfani da bayanin hangen nesan ka da dabi'u. dabi'un Ikilisiya yakamata su taimaka wajen ginawa da jagorancin tsarin almajirantarwa.

a. Ka Koya musu yadda za su karanta Littafi Mai Tsarki da kansu.
b. Ka Koya musu yadda za su yi bincike da kuma addu'a ta hanyar Littafi Mai Tsarki.
c. Ka Koya musu yadda za su yi addu'a da kuma magana da Ubangiji. (Matta 6:5-13).
d. Koya musu muhimmanci da darajar daukaka Ubangiji da zakka.
e. Ka Koya musu manufa ba da da baiko ga Ubangiji.
f. Ka Koya musu aiki na musamman na iyali da kuma lafiyayyen aure da ta mika kai ga Allah.
g. Ka yi anfani da damarmaki na koyarwa don ka yi murna, ka horar ka kuma karfafa su (Luka 10:17-20).

D. Ka fara Tsarin ka ta almajirtarwa da Sanin yadda zai kasance a ƙarshe a zuciyar ka, yi la'akari da abin da kake gani a matsayin mutum wanda ya manyanta a ruhaniya.

bayyana da kuma ayyana yadda wannan mutumin zai kasance.  daga wannan ma'anar fara gina tsari wanda zai taimake ka wajen jagorantar sabon mai bi daga rashin balaga zuwa ga manyanta.  yi la'akari da zaɓuɓɓukan da ke sama, amma kuma ka nemi Ubangiji kuma ka roƙe shi ya yi muka jagora wajen ƙirƙirar tsari na musamman na almajiranci ga Ikilisiyar ka.

**KA MAIMAITA WANNAN TSARI SAU DA YAWA YADDA ZAI YIWU**

A. Kafawa da kuma ninka (ribambanya) almajirai da majami'u ya kamata a sanya su cikin aikin kowace Ikilisiya. Dokar mallaka da aka ba Adamu, da kuma alkawarin da Allah ya yi da ibrahim yana buƙatar matsayi da hali na ninkawa(hayyayafa). Ikklisiya da muminai ba a keɓe su daga wannan umarni ba.

B. Ka tabbata kana neman Ubangiji domin samun sabon hange, hikima da kuma bishewa sa'ad da ka ke maimaita tsarin da kuma horas da wasu don su yi haka. Yayin da kake samun karuwa (hayyayafa), za'a bukaci a saka sababbin shugabannai don su shugabantar su kuma girma. Mai yiwuwa ne sababbin shugabannin da ka horas da Kuma saka su wurin hidima su dauki tasirin hidimarka. Yi farin ciki da wadannan da suka yi nasara cikin shirin Allah!

C. Salon ribanbanyawa da kuma almajirtarwa da Manzo Bulus ya karfafa ya kunshi tsarraraki guda hudu ko fiye. (2 Tim. 2:2).
    1. Bulus (Tsara na 1) zuwa ga Timoti (tsara na 2)
    2. Timoti zuwa ga amintattun mutane. (Tsara na 3)
    3. Amintattun Mutane zuwa ga wasu. (tsara na 4)

D. Dalilai masu dacewa a aikace na maimaita da sake fasalin tsarin.
    1. Kafa sabuwar ikilisiya tsari ne mafi alfanu na yin wa'azin bishara. Bisa ga kididdigar mutane na iya amsawa da yawa zuwa ga taron wa'azin bishara, har yanzu zuwa 80% daga cikin 100 na mutanen su na barin imanin su (bangaskiya) idan ba a hada su an kumashigar da su cikin ikilisiya ba. Domin haka ikilisiya wanda take da kungiyar fitan bishara mai karfi ita ce tsari mafi anfani na wa'azin bishara.
    2. Sabuwar ikilisiya tana ba da wuri na taimakawa da kuma shayar (ciyar) da wadanda ke cikin bukata. Ikilisiyoyi su yi shelar albishir mai dadi, yanci ga daurarru su kuma taimaka wa wadanda a ka danne (Luka 4:18-19). Ko da yake kai wa mutane taimako don biyan bukatun su ya zama dole da kuma muhimmanci, ba ta maye gurbin bukata don shaida Bishara

ba! Matsayin ruhaniya na jama'a ya fi muhimmanci fiye da komai (Markus 8:36).

3. Ikilisiyar da ke nan tuntuni tana ba da kafuwa da kuma kayan aiki wa sabobin ikilisiyoyi. Da zarar sabuwar ikilisiya ta kafu, an sanya ta don ta fara kafa wasu sababbin ikilisiyoyi kuma za ta zama kaffafen wuri mai karfi domin Mulkin Allah.
4. Kungiyar shugabanci da ke nan tuntuni na iya yin addu'a, taimako, hikima da kuma bada shawarwari ga sabuwar ikilisiya da a ka kafa. Kamar yadda iyaye ke horas da 'ya'yansu don shiga duniya, sabuwar ikilisiya na iya dogara ga wadda take nan tuntuni domin samun bishewa da tallafawa. Dukan ikilisiyoyi su shirya don su zama iyaye na ruhaniya ga sababbin diyar ikilisiyoyi a kullayomi.
5. Ribambanya ikilisiyoyi yana motsa sha'awar ruhaniya da sa yanki zumudi. Jama'a na yin murna game da sababbin abubuwa, kuma a matsayin masu bin Kristi wannan takamaiman gaskiya ce. Sabuwar ikilisiya da a ka kafa za ta kawo ci gaba ga al'umma kuma za ta kawo sauyi a yanayi na ruhaniya.
6. Hayayyafawa na kaiwa ga ribambanyawa, wanda yafi muhimmanci sosai a girma fiye da ƙari. Ribambanyawa ta na zuwa daga tunkara mai amfani, neman hanyoyi na kara yin tasiri ta fadadar hanya. Yaduwa abu ne mafi sauki sa'adda dukan membobin kungiya sun karfafu don su shiga cikin bangare na yin tasiri domin yi wa Ubangiji aiki.

## XI. MANYAN ABUBUWA GUDA 10 NA GUDANAR DA KAFA IKILISIYA

(Lokacin koyaswa mintoci 30)

1. **Addu'a** – Rayuwar jazircewa ga yin addu'a na shugabanai an maida ta ga sababbin shugabannai da a ka almajiratar da su. Addu'a ita ce tushen iko daga wurin Allah. Idan ba tare da addu'a ba, shugabannai za su kare cikin Rashin nasara, kuma ikilisiyar da suke shugabanta za ta ruguje (gurgunta).
2. **Yalwar Shuka bishara** – Wa'azin bishara ya wajaba ta kasance a dukan abin da za ka yi. Ana Shaidar ikon canjin rayuwa na bishara ma marasa bi. Shaida na alheran Allah, tanadin sa, ikon warkaswa, karfafawa har ma kuma da horo zasu karfafa duk batattu da waɗanda suka tsira. Wannan na shaida ci gaban Allah da ma'amala da 'yan adam a akai-akai.
3. **Da Niyya (da gangan)** – Ana kafa ikilisiyoyi da gangan da kuma manufa. An fara kuma ana kiyaye dabarun kafa Ikilisiya tare da ɗabi'a da tsari mai fa'ida. Haɓaka sabbin shugabanni, niyyar sabbin yankuna/wurare da ƙaddamar da sabbin majami'u, tsari ne na niyya mai gudana wanda ke bin tsari da dabaru.
4. **Ikon Nassi -** Littafi Mai Tsarki shine tabbataccen tushen jagora don koyaswa, aiki, da kuma rayuwa kanta. Nassi dole ne ya kasance na tsakiya. Ficewa daga nassi zai haifar da rashin aiki da sauri, bidi'a da gazawa.
5. **Shugabancin gida:** jagoranci mai karfi na gari. Dole ne kowace shukar Ikilisiya ta haɓaka kuma ta ɗaga (tada) shugabanni a cikin kanta. dole ne shugabanni su jagoranci kansu da kyau, ta yadda za su iya jagorantar wasu da kyau.
6. **"Shugabanci mai ƙarfi"** – ana ganin duk membobi a matsayin 'masu hidima' na bishara. Babu rarrabuwa na duniya da tsarki. Afisawa 4 ta bayyana sarai cewa kowa ya kamata ya shirya don aikin hidima. wannan ba yana nufin cewa duka za mu zama ministocin cikakken lokaci ba. akasin haka, ya kamata dukkan mutane su zama ministoci a fagen tasirinsu. Awatarda da sauyi a waɗannan fannonin tasiri daban-daban zai ba da damar Ikklisiya ta haɓaka cikin sauri.
7. **Ikilisoyi na rukuni**– ba a bukatar gini don zaman ciki. Ikilisiyar sun mai da hankali kan wayar da kan jama'a. yawancin ayyukan hidima suna faruwa a wajen ginin ko wurin taro. Isar da sako bayyananniyar aikin Yesu ne, da kuma nunin babban umurni da ake yi. Isar da sako ba ya faruwa a tsakanin bangon Ikilisiya, dole ne ya faru a inda mutane suke.
8. **Ikkilisiyoyi dake kafa ikikilisiyoyi -** haifuwa yanayin halitta ne kuma wani bangare ne na isa ga mutane da yawa. Ƙungiyoyin kafa Ikkilisiya suna ci gaba da

ƙwazo ta hanyar sanya DNA na haifuwa.  babu wata majami'a da ke da niyyar ba za ta haifuwa ba, kuma wannan bai kamata ya zama abin la'akari ba.

9. **Saurin haifuwa –** gaggawar isar da mutane ga Kristi .  Ya kamata mabiyan Kristi su fito da gaggawa domin ɓatattu.  Wannan zai bayyana a cikin saurin haifuwar ikkilisiyoyi da kuma tirjiyar Kai bishara.
10. **Ikkilisiyoyi suna da lafiya** – majami'u masu lafiya koyaushe suna da dalilai guda biyar: sujada;  isar da bishara da na mishan;  ilimi da almajirantarwa;  hidima;  da zumunci.  Wadannan mahimman dalilai za su sa Ikklisiya ta kasance da lafiya, mahimmanci da girma.  Waɗannan mahimman dalilai kuma suna haifar da yanayi da hali na haihuwa( ribambanyawa).

## XII. ANA WAKILTAR IKILISIYA A FAGEN KASUWA

(Lokacin koyaswa mintoci 45)

* Mafi dacewa a cikin birnane ko cibiyoyin tattalin arziki masu tasowa na kasuwanci.

Fastoci da kuma shugabanan ikilisiya suna da muhimmiyar rawa da za su taka don shiryawa su kuma almajirtar da maza da mata a wurin kasuwa su kuma yi tarayya da su don su zama masu kawo sauyi. Ikilisiya ta wuci taron ranan Lahadi kadai. Ikilisiya rayyace, tana aiki kowace rana kuma ya kamata a wakilce ta a duniya ta wurin dukan mabiyan Kristi.

A. Muhimmancin karfafa ikilisiya a wurin Kasuwanci

**Ma’anonin wurin Kasuwa:**

- Kasuwa wurin hada-hadar kasuwanci ne, ilimi, da kuma gwamnati. A fadada ma'anar, kasuwa ta na kusan ko’ina a wajen ginin Ikkilisiya.
- Kasuwa mazauni ne na iko da kuma hukuma (mulki) inda sauyi na al'umma na iya faruwa.

**Muhimmancin fagen kasuwa**

- An ba mu takamaiman umurni daga Farawa 1 don mu mallaki Danuya. Wannan dokar mallaka ya wajaba don kula da dukkan abubuwa saboda daukakar Allah har yanzu yana kan aiki kuma ta shafi wurin kasuwa. Farawa 1:28-30
- An ba mu Babban Umarni: kuma an umurcemu cewa mu almajirtar da dukan al’ummai. Matta 28:18-20, Markus 16:15).
- Aiki Ibada Ne: idan wani yana aiki a kasuwa don daukakar Allah, aikinsa/ta na da TSARKI! A.W. Tozer: “Ba ABIN DA mutum ya ke yi ba amma ME YA SA ya ke yin hakan ne ya sa aikinsa ya zama na duniya ko Kuma mai tsarki”

**Bangarori Takwas na Tasirin al’ada**

Wadannan bangarori guda takwas na yin tasiri suna wakiltar abubuwa na tushen kowace al’umma ko al’ada. Kowane fanni na tasiri yana tsara tunani da Hangen nesa na mutanen da ke cikin wannan al’umma. An kira mu don mu zama da tasiri a kan al’ada, amma wadannan abubuwa na al’umma Kuma suna shafar masu bi .ko yanayin tasirin na Allah ne ko a'a ya dogara da waɗanda ke da mulki da iko akan waɗannan tsaunuka.  dole ne mu tayar da shugabanni na Allah don su yi tasiri a wadannan bangarorin:

1. Gwamnati
2. Iyali
3. Ilimi
4. Ikilisiya
5. Sashen Sadarwa
6. Fasaha da Nishadi
7. Kasuwanci
8. Kimiya da Fasahar kere-kere

Tattalin arziki shi ne na’urar da ke gudanar da dukan wadannan bangarori guda takwas na yin tasiri. Yana da muhimmanci a sami shugabannai na wurin kasuwa masu tsoron Allah da za su tuka wannan injin din. Shirin Allah ne kome ya shafi dukan duniya. Yana amfani da duniya duka don ya hada mutane ta hanyoyi wanda ba a taɓa jin irinsa ba. Akwai babban zarafi na yin tasiri.

B. Fastoci masu shiryawa ne kuma ikilisiya cibiya (wuri) ce na shiryarwa.
   1. Ikilisiya cibiya ce na shiryarwa. Babban aiki na Fastoci da kuma masu koyarwa ita ce su “shiryar da jama’ar Allah domin ayyukan hidima”. (Afisawa 4:11-13).
   2. Kasuwa fili ce na aikin bishara! Ta wurin horas da ‘yan kasuwa fastoci za su iya fadada mulkin Allah sosai. Bisa ga kididdiga, ‘yan kasuwa sukan sadu fuska da fuska da batattun mutane da yawa a kowace mako fiye da fasto.
   3. Anfanin ya isa girbi, amma ma’aikatan kadan ne (Luka 10:2).
   4. Burin ita ce a shiryar da shugabanai a cikin ikilisiyoyinmu wadanda za su iya yin aiki da kiran da aka yi musu su kuma fadada mulkin Allah a cikin ikilisiya, al’umma, wurin aiki, da kuma duniya. A shirya su don su zama masu shiryawa, almajirtad da don su ma su almajirtar.
   5. Hadin kai da ikilisiyar gida ya kamata ya haifar wa masu bi damar samun kayan aiki na ruhaniya don kammala aikin canza al’umma domin daukakar mulkin Allah a wajen ginin ikilisiya. Ka yi la’akari da matakin ka na almajirtarwa a matsayin zarafi da zaka shiga Tsari da kuma shiryar da masu bin Yesu domin su Zama da anfani a bangarorin su na tasiri.

      Dukan bil'adama suna tarayya kan wadannan tambayoyi:
      - Ta yaya zan tanada wa iyalina?
      - Ta yaya zan yi rayuwa cikin kwanciyar hankali da tabbacin kariya ga iyali na?

- Ta yaya zan kasance da dangantaka mai ma’ana?
- Ta yaya Tsarin da nake rayuwa aciki zai iya samarda tsaro, adalci da kuma zarafi na tattalin arziki?

Shugabannin yan Kasuwa na mulkin Allah za su kasance da shiri don su taimaka wajen bada amsoshi ga wadanan tambayoyin. Shi ya sa a ke tada shugabanai masu tsoron Allah. Tada ƙwararrun shugabannin kasuwanci ('yan ƙasa) yana da mahimmanci.

C. Yadda za a shiryar da shugabanni ‘yan kasuwa a cikin ikilisiya.

A Koyar da shugabanni ‘yan kasuwa su zama masu kamun kifi (masuntan mutane).

A cikin kamun kifi, yana da muhimmanci a yi amfani da koto (dubara) da ta dace. Kifi ba za su sauya halin cin abincin su ba. Kristoci dole ne su nuna yadda za a yi rayuwa ta nasara a cikin duniya. Al’amuran tattalin arziki hanya ce da ta hada duniya baki daya za a iya amfani da damar don Isa ga mutane. Ya zama wajabi mu yi anfani da kalmar Allah a zahiri a bangarorin mu na tasiri.

Yayin da Ikkilisiya ta horas da dan kasuwa kuma ta bashi kayan aiki, zai iya kamun ‘kifi’ yadda ya kamata a Kasuwa. A horas da shugabannai ‘yan kasuwa su kasance da nazari bisa ga Littafi Mai TSarki a kan tambayoyi da ya shafi rayuwar yau da kullum na dan Adam da za’a iya tunkararsu da shi.

A Inganta akuma yi koyaswa game da hidimar wurin Kasuwanci. (kudi, rashawa, dangantakar adalci da kuma shugabanci):

- Daga bagadi
- A kananan Rukunoni (kungiyoyi)
- A cikin al’umma.

**A Inganta a kuma Karfafa kira ga yin kasuwanci:**

- Taimaki ‘yan kasuwa su ga aikinsu a matsayin hidima.
- Karfafa su su sa “tsarin hidima” a cikin shirin kasuwancinsu.

- Yi wa’azin rukunin aiki a matsayin ibada daga bagadi da kuma a kananan rukunoni.
- A Dibiya hannuwa a kan shugabanni ‘yan kasuwa a sa su ga yin aiki.

**A matsayinka na fasto ko shugaba na hidima, ka yi kokarin gina danganta:**

- Ka Zabi shugabanni kadan ‘yan kasuwa su rika haduwa da kai a kullayomi ( akai-akai).
- Ka Sadu da su daya bayan daya a wurin kasuwancinsu (Yesu ya tafi inda almajiran su ke a lokacin da ya kira su).
- Ku Tattauna ku kuma yi binciken kafofi da ya dace da wurin kasuwanci.
- A Taimaki shugabannin wurin kasuwa su gani, su yi tunani, su kuma yin tsari na tsararaki da yawa.

**A yi Koyi daga wurin shugabannin kasuwa:**

- A ba da dama domin su tofa su kuma fadi ra’ayoyinsu da suka danganci gudanar da ikilisiya.
- A gudanar da kasuwanci na ma’aikata ko ikilisiya da mutunci; a kula da kudade da kuma mutane da kyau.

**Abubuwa da kuma halaye da za a guje wa:**

- Daukar ‘yan kasuwa a matsayin “rajistar karban kudi”.
- Daukar ’yan kasuwa a matsayin wani mugun abu ko yan duniya.
- Duban kudi a matsayin rashin tsoron Allah.
- Guje wa ’yan kasuwa.
- Zama mai karya ko magudi.

D. Muhimman Sakamako da za'a iya sammani (sa zuciya).

1. Jama’ar Allah za su fara kafa Mulkin Allah a bangarorin su na tasiri – a wajen Ikilisiya.
2. Za’a kafa Kasuwancin mulkin Allah da yawa a duniya.
3. Za a samar da sabobin jari (kudi) ta wurin Jama’ar Allah domin manufofin sa.
4. Ikilisiyoyi da suka zama cibiyoyin shiryarwa za su ga:

a. Balagar masu bi.
b. Yunkurin almajirtarwa a wurin aiki.
c. Suna Tasirin da ya dace a garruruwansu da kuma cikin al'ummonin su.
d. Wadanda suka bace sun dawo a cikin Ikilisiya.
e. Ayyukan Mulki da suka wuce kusurwowi hudu na ginin majami'a.
f. Girma a yawan jama'a da kuma kudade.
g. A tsawon lokaci, matakin 'babban jari na ruhaniya' zai karu a cikin al'umma (aminci, adalci, tsarki, wadata)

5. Mai kafa ikilisiya an kira shi ne don ya shiryar da dukan masu bin Yesu da gaskiya ta ruhaniya wadda ke bamu damar zama ingantaccen gishiri da kuma haske a duniya.
    - Ka mika kai ga yin wa'azi da koyaswa akan kasuwanci, kudi, da kuma aiki daga kan bagadi na ikilisiya.
    - Ka mika kai ga almajirtar da rukunin shugabannin 'yan kasuwa a ikilisiyarku.
    - Ka mika kai a gudanar da kasuwanci na ikilisiyarku ko hidima da aminci da kuma neman shawara daga shugabani 'yan kasuwa a ikilisiyarku.
    - Ka kebe shugabannin kasuwa don su dauki Bangarori Bakwai na yin tasirin Mulkin Allah.

## Back Cover

Ka himmantu, ka mika kanka yardajje ga Allah, ma'aikaci wanda ba hanya ya kunyata, mai kuma fassara Maganar gaskiya daidai.

2 Timoti 2:15.

Jerin **Littafin Kafa Ikilisiya** an kikrkira don taimakon masu hidimar bishara su zama yardajjen ma'aikata domin Yesu Almasihu da kuma ikkilisiyar Sa. An bunkasa a matsayin saikon nazari na Kanka saboda rayar (bunkasa) Kanka da kuma ma'aikata, wannan kayan aiki mai daraja ta ba ka taimako a aikace saboda girma a matsayin mai bin Yesu Almasihu da kuma mai hidimar Albishir Mai dadi na Yesu. Wannan littafi an tsara musamman saboda shugabanai fastoci a kasashe da suka bunkasa wadanda suke hidimtawa a gaba gaba na bisharar Global Advance.

Jerin **Littafin Kafa Ikkilisiya** an wallafa ta daga Global Advance. Wannan ma'aikata na dukan duniya ta tanadi horaswa, kayan aiki da kuma karfafawa domin shugabanan ikkilisiya a kasashe da yawa. Don Karin bayani a ziyarci yanar gizo na Global Advance a www.globaladvance.org da kuma www.2tim2.org

**GAME DA MAWALLAFI:**

David Shibley ya kafa Global Advance, ma'aikata da ke shiryar da dubban fastoci da kuma shugabanan 'yan kasuwa a kowace shekara don su cika Babban Umurni.

Litattafan David Shibley za a iya saye (samu) a layin yanar gizo a: www.globaladvance.org